



# MUJALLAR CITAD RADIO

## RADIYON DA ZAKU SAURARA

www.citad.org/radio

Volume 1, issue 4

09-10-1442 AH
21-05-2021 AD



***CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA***

## LABARAN CIKI


| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |


**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

## Sai an yaƙi cin hanci da rashawa sannan za a samu nasarar magance ƙalubalen tsaro a Najeriya – CITAD

Babban daraktan Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa da Cigaban Al'umma CITAD, Mallam Yunusa Ya'u ya bayyana cewa yaƙi da matsalar tsaro da gwamnatin tarayyar Najeriya ta ke yi ba zai taɓa yin nasara ba muddin akwai cin hanci da rashawa a tsakanin ma'aikatu da jami'an gwamanati.

Malam Yunusa Ya'u ya bayyana hakan ne a yau Alhamis a lokacin da ya ke gabatar da wasu littafai da cibiyar ta wallafa. Littattafan da su ka haɗa da The Compromised State: How Corruption Sustains Insecurity in Nigeria" da kuma Context and Content in Hate Speech Discourse in Nigeria".

Littattafan da aka rubuta su cikin harshen Ingilishi, inda littafi na farko ya mayar da hankali ne akan yadda cin hanci da rashawa ke ƙara rura wutar rikicin da ke faruwa a Najeriya, sai kuma dayan wanda ya mayar da hakali akan illar da kalaman batanci kan haifar a cikin al'umma tare da kawo tashin – tashina.

Babban daraktan ya ce kalaman ɓatanci da cin hanci da rashawa su na ƙara rura wutar rikici a Najeriya, kuma abu ne mai wahala a samu nasara akan yaƙin da ake da ayyukan ta'addanci muddin ba a yaki wadannan abubuwa ba to abu ne mai wahala a samu zaman lafiya da cigaba.

Malam Yunusa Ya'u ya ce a sakamakon cin hanci da rashawa a ɓangaren tsaron kasar nan ya sanya masu riƙe da ɓangaren ke burin ganin an cigaba da samun rashin kwanciyar hankali domin kawai su dawwama akan shugabancin.

Hakazalika, babban daraktan ya ce al'amarin yaƙi da cin hanci da rashawa bai kamata ya zama aikin gwamnatin tarayya kaɗai ba, ya kamata jihohi su kasance suna taka rawa wajen yaƙi da wannan mummunar ɗabi'ar.

Haka kuma ya buƙaci masu riƙe da mukaman gwamnati da kuma jagororin al'umma da su yi ƙokari su karanta wadannan littattafai domin hakan zai sanya musu karsashin yaki da cin hanci da rashawa.

A ƙarshe ya yi kira ga kafafen yaɗa labarai da kungiyoyin sa kai da su himmatu wajen zakulo abubuwan da za su wayar da kan al'umma akan haɗarin da tattare da cin da rashawa tun daga tushe.


## Hotunan Taron Kaddamar Da Wallafar Citad Ga 'Yan Jaridu



# Taron Bayar da Horo Na Musamman kan Hakokin Mata da Kula da Cin Zarafin Su, Karo Na Uku.

A kakokarin ta na ganin tra magance cin zarafin mata da tsangwama a shafukan intanet, da cike gibi da ke tsakanin su da maza, Cibiyar Bunkasa Fasahar Sadarwa da Cigaban Al'umma (CITAD), zata bada horo na tsawon kwanaki biyu akan wannan al'amari.

Taron mai taken **Bauchi Feminist Internet School**, zai gudana ne a jihar Bauchi na tsawon kwana biyu. Ga wanda basu samu dammar shiga ba zasu iya bibiyar taron a kafafen sadarwa na zamani na cibiyar bunkasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma.




## Ilimin 'Ya Mace
## Daga Gazzali Haruna Ibrahim

Shirin ilimin Ya mace shiri ne dake maida hankali kan abubuwan da suka shafi rayuwar ilimi musamman ma na mata , da hanyoyi da kuma dabaru dan ganin an inganta ilim.

Ilimin 'Ya Mace na wannan makon ya samu bakuncin Ibrahim Salisu Sani Mataimakim shugan makarantar, Al-muhajirun Islamiyya Wanda muka tattauna akan Gudummawar Matasa akan Ilimin Mata II.

.






## Daga 'yan jaridu.

Shirin daga yan jaridu na wannan makon ya karbi bakonci mallam Abubakar Muhmmad Umar, wanda yake ma'aikacine da gidan jaridar Daily Trust, sannan dan jarida ne mai aiki da sabbin kafafen sadarwa na zamani wajen gudanr da aiyukansa.

Shirin na wannan makon ya maida hankali ne kan irin rawar da labaran karya yake takawa wajen haifar da rikici a tsakanin al'umma.



matsalar tasiri ko yaduwar labaran karya na kara ta'azzare yayin da 'yan jarida ke yin lalaci wajen neman labara"



WWW.CITAD.ORG/ RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

www.citad.org

**Center For Information Technology and Development**

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

## Jadawali Ayyukan mu a Makon da ya gabata

1.Event: CITAD Goron Sallah
Topic: Call upon ICT Skills for the Betterment of our Future.
DATE: Thursday, 20th May 2021.

2. Event: CMC Training for Staffs
Venue: CITAD Office Abuja
Date: Monday 17th May, 2021

3. Event: Advocacy Visit to NHRC on Land Grabbing.
Venue: NHRC Headquarters Abuja
Date: Tuesday, 18th May, 2021

4. Program: Ilimin 'Ya Mace Radio Program
Guest: Ibrahim Salisu Sani Assistant Head Teacher, Al-muhajirun Islamiy-ya.
Topic: Gudummawar Matasa akan Ilimin Mata II
Date Wednesday, 19th MAY, 2021

5. Program: Muji daga Jaridummu
Guest: Abubakar Muhammad Usman (Daily Trust Multimedia Journalist)
Topic: Illar Labaran Ƙarya Wajen Ƙara Haifar da Rikici
Date: Wednesday, 19th May - 2021

6. Program: SIYASA DA RAYUWA.
Guest: Suhail Abdullah
Topic: Amfani da fasahar sadarwa wajen yin tsaftacecen zabe
Venue: CITAD Online Radio
Date: Thursday, 20th may, 2021

7. Event: Media Presentation of New Books
Venue: CITAD, Kano
Date: Thursday, May 20, 2021

7. Program: Twitter Chat on Covid19
Topic: Radio as a Tool for Creating Awareness on Covid19 Vaccines
Guest: Dr Abdul Hamidu Abdullahi, Senior Lecturer, Department of Local Government & Development Studies. Ahmadu Bello University, Zaria and Presenter, DITV/Albarka Radio, 97.7FM Zaria
Venue: Twitter
Date: Friday 20th May, 2021